# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Ni ma ɗan Adam ne: 'Yan Afirkan da ke fama da taɓin hankali
## Kashi na biyu: Kukan zuci

Wanda ya rubuta: Chrispin Mwakideu
Wanda ya fassara: Yusuf Idris
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**'Yan Wasa:**

John: ɗan shekara 25
Jane: 'yar shekara 25
Amina: 'yar shekara 19
Dije: 'yar shekara 19
Duduwa: 'yar shekara 35
Musa: ɗan shekara 16
Jummai: 'yar shekara 40

**Mai gabatarwa:**

Masu sauraronmu, barkanmu da sake kasancewa da ku a cikin kashi na biyu na shirinmu na “Ji Ka Karu” wanda muke kawo muku a kan mutane masu taɓin hankali a ƙasashenmu na nahiyar Afirka. A cikin shirin na farko, an kori John daga aikin da yake yi a Shagon Na Kowa. Amina, ɗalibar nan mai koyan aikin nas, ta nuna wasu halaye na dabam a lokacin da suke cin abinci da ƙawarta a ɗakin cin abincin makarantarsu. A can ƙauye kuma Duduwa na iya bakin ƙoƙarinta na ganin cewa ta kori aljanun da suka kama ɗanta. To daga nan ina labarin zai kai mu? A kasance a cikin shirin mai taken “Kukan Zuci”. Za mu faro ne daga lokacin da John ya koma gida ba lokacin da ya saba komawa ba. Matarsa Jane, wadda a yanzu haka tana da juna biyu, na jiranshi a gidan.

**Fitowa ta 1: A gidan John**

**Jane:** John! Ka dawo gida da wuri yau. Ka ƙosa ka gan ni ne haka?

**John:** A’a, ba ni na yi ba…

**Jane:** Ba ka ƙosa ka gan ni ba? Ai kuwa da haushi saboda ni na ƙosa ka dawo.

**John:** Ba ni na yi ba, ba kya jin abin da na ce ne? Ba ni ba ne! Ba a yi daidai ba, wannan bai kamata ba!

**Jane:** John, lafiya dai? Me ya faru ne da kai? ... Wooi, kar ka yi fushi! Ka yi hakuri. Ka yi hakuri in na yi wani abin da ya ɓata maka rai ne.

**John:** Ba ni ba ne, wallahi ba ni ba ne!

**Jane:** John, ka yi shiru don Allah. Ban san abin da ya faru ba, amma ni na yarda da kai. Ban taɓa ganinka a cikin irin wannan halin ba. Kana ba ni tsoro kuma ka san ina da ciki. Yanzu dai don Allah ka kwantar da hankalinka, kuma ka faɗa min abin da ya faru da kai har ya sa kake kuka?

**John:** Ni ki ƙyale ni! Don Allah ki ƙyale ni kawai, Jane. Ina buƙatar lokaci don in yi nazari a kan wannan abin. Ki yi haƙuri amma ban san ma irin bayanin da zan yi miki a kan al'amarin ba. Ki ba ni ɗan lokaci kaɗan.

**Jane:** John, cikin 'yan watannin nan ne fa kawai muka yi rantsuwa cewa za mu riƙa tsayawa ga juna a irin duk halin da muka samu kanmu, mai daɗi ko marasa daɗi. Me zai hana ka faɗa min? Mmm, ni fa yanzu matarka ce. Muna buƙatar taimaka wa juna.

**John:** A'a, Jane! Ki kula kawai da kanki da kuma 'yar. Ni kuma zan kula da kaina. Ki yafe min, amma ina buƙatar in samu lokaci wa kaina.

**Jane:** Amma Maigida, ka …

**John:** Don Allah ki ƙyale ni haka! Ina buƙatar in ɗan kwanta. Wataƙila hakan yan ɗan samu natsuwa.

**Jane:** Shi ke nan, na bar ka.

**Mai ba da labari:**

Haka dai Jane cikin mamaki ta sa wa maigidanta ido wanda ya kasance mai raha da walwala, ya kwanta a gado ba tare da ya ƙara cewa uffan ba. Tambayar da ke damunta a zuciya ita ce: me ya faru da ya sa John ya canza

halinshi a cikin ɗan ƙanƙanin lokaci? Yanzu bari mu bar ta a cikin tunaninta, mu koma makarantar koyon aikin likita inda Amina da Dije suka koma ɗakinsu bayan sun kammala darussansu.

**Fitowa ta 2: A makaranta**

**Dije:** Amina, haba, ki tashi ki taka mana! Ki daina ɗaure fuska mana haka. Haba Amina! Ke, kin ma san wani abu ne? Muna buƙatar shaƙatawa, ya kamata mu je *party* yau. Ko yaya kika ce, Amina? Haba, tashi mana mu taka!

**Amina:** Ki kashe rediyon.

**Dije:** Me ke damunki ne? Da kikan so ki ji maganar rawa. Haba, ki tashi ki ɗan taka mana, Amina! Tashi mana!

**Amina:** Ki kashe rediyon na ce!

**Dije:** Me kika ce? Ban ji ki ba. Ki yi magana da ƙarfi, Amina!

**Amina:** Na ce, ki kashe rediyon!

**Dije:** Shi ke nan, shi ke nan, na ji. Ai ba sai kin yi ihu haka ba sai ka ce mahaukaciya. Yanzu kuma sai me? Ba kiɗa, ba …

**Amina:** Ssssh! Suna nan. Suna nan kuma suna so su ɗauke ni!

**Dije:** Amina, ki daina wannan wawancin da kike yi mana. Ba kowa a nan wurin in ba ni da ke ba kawai. Me kike sha ne? Koma ma me kike sha, to bai karɓe ki ba.

**Amina:** A'a! Ba za ku ɗauke ni ba! Ba zan yarda ba! Kar ku zo kusa da ni! A'a! Ku ƙyale ni na ce!

**Dije:** A'a, ikon Allah! Amina, na lura ba wasa kike yi ba. Na lura taɓin hankali ne ya kama ki! Ya kamata in nemi taimako. Ina zaune da mahaukaciya ban sani ba.

**Amina:** Don Allah kar ki tafi. Idan kika ƙyale ni za su tafi da ni. Ki tsaya tare da ni. Tsoro nake ji. Don Allah kar ki tafi.

**Dije:** Shi ke nan, Amina, sake min hannu, ba zan tafi ba, na yi miki alƙawari. Sake min hannuna a hankali.

**Amina:** Na gode, na gode. … A'a! Ki buɗe ƙofar nan don Allah.

**Dije:** A yi taimako! Wani ya taimake ni!

**Mai ba da labari:**
Dije ta fara matuƙar tsoron ƙawarta Amina, a yayin da ta ruga da gudu tana neman agaji. Yawancin mutanen nahiyar Afirka, har da waɗanda suke ɓangaren kiwon lafiya, ba su fahimci yadda taɓin hankali yake ba. Yawancin jama'a na tunanin cewa, aljanu ne suke kama masu taɓin hankali, ko kuma an tsine musu ne saboda sun yi wani mugun abu. Me zai samu Amina? Amma yanzu bari mu koma ƙauyen inda Musan nan mai taɓin hankali yake fama da masassara. Mahaifiyarshi Duduwa sai ta yanke shawarar ta kai shi ɗakin shan maganin da ke ƙauyen. A nan ne kuma ta haɗu da Jummai.

**Fitowa ta 3: A asibiti**

**Duduwa:** Sannunku! Don Allah, yarona yana buƙatar ganin likita, jikinshi ya yi zafi sosai. Na yi duk abin da zan iya yi amma zafin sai ƙaruwa yake yi.

**Jummai:** To shi ke nan, shekarun ɗanki nawa?

**Duduwa:** Yanzu shekarun Musa goma sha shida. Nas, don Allah ki yi wani abu, ciwon kam na damunshi sosai.

**Jummai:** Sha shida! Amma sai ka ce ɗan shekara bakwai! Me ya sa ba ya girma? Me kuma yake damunshi?

**Musa:** Kai… kai… Mama… kai…

**Duduwa:** Nas, don Allah ki yi wani abu, ciwon kai yana damunsa sosai. Bai cika yin irin wannan rakin ba!

**Jummai:** Malama, kafin ya ga likita, sai na san ko da can yana da wani tarihi na wani ciwo. Tabbas akwai wani abin da yake damunshi. Yana da ciwon hauka ne? Ina nufin yana da taɓin hankali?

**Duduwa:** Musa ba mahaukaci ba ne. Aljanu ne kawai suke damunsa lokaci-lokaci. Bayan wannan ba wani abin da yake damunsa.

**Jummai:** Don Allah ki ce mishi ya rufe bakinshi! Muna da wasu marasa lafiyan a nan. Tsaya ki ji. Ki yi hakuri, amma ba wani abin da za mu iya yi miki a nan. Ɗanki na buƙatar kulawa ta musamman ne, kuma mu ba mu da irin kayan aikin a nan. Ina ba ki shawarar ki kai shi babban asibiti, wataƙila za su iya taimakonshi a can.

**Musa:** Aaa… uhmmm… A…

**Duduwa:** Ssssshh! Amma ina so a ba shi maganin masassarar da ke damunshi ne kawai! Ba ni da kuɗin maganin, shi ya sa. Ta yaya zan iya zuwa birni? Ko nan da na zo sai da na shafe tafiyar awa ɗaya. Nas, don Allah ki taimaka mana! Ba kya ganin irin wahalar da yake sha?

**Jummai:** Kwarai ina gani mana, amma kamar yadda na ce, ba za mu iya kula da masu ciwon hauka ba, masu ƙananan cututtuka ne kawai muke duddubuwa a nan. Ya kamata a ce ɗanki yana wata cibiya ta kula da masu taɓin hankali. Ki yi haƙuri, amma ya kamata ku tafi. Ɗanki na tsoratar da sauran marasa lafiyan da ke nan, kuma mu ba ma son wani abu ya faru.

**Duduwa:** Ɗana ba ya aikata wani mugun abu! Ba abin da zai yi wa kowa.

**Jummai:** Abin da ba na so ke nan. Don Allah ki ɗauke shi daga nan. Ya kamata ki kai shi asibitin mahaukata.

**Duduwa:** Ɗana ba mahaukaci ba ne! Sau nawa zan faɗa miki haka? Zo mu koma gida, Musa. Na kai ka wajen mai maganin gargajiyan nan Maude. Ko banza yana da tausayi.

**Mai ba da labari:**

Duduwa ta yi gaskiya. Yawancin ɗakunan shan magani na ƙasashen Afirka ba sa nuna tausayi ga mutanen da ke fama da ciwon taɓin hankali. Wani bincike da aka yi ba da daɗewa ba, ya nuna cewa ƙasar Guinea Bissau ba ta da likitan mahaukata, ba su da ƙwararren likitan da zai iya gane ko mutum yana da cutar hauka, ko kuma ƙwararrun da suka ƙware a kan ƙwakwalwa. Kasar Liberia na da ƙwararren likita ɗaya ne kawai a kan ƙwakwalwa, sannan kuma akwai ƙasashen da ba su da asibitocin kula da masu taɓin hankali, duk kuwa

da cewa Kungiyar Lafiya ta Duniya ta yi ƙiyasin cewa kimanin kashi tamanin na mutane masu taɓin hankali na zaune ne a ƙasashe masu tasowa. Ba sa samun wani kulawa, inda kuma suke samu, to bai taka kara ya karya ba. A yayin da Duduwa ta ɗauki ɗanta don ta kai shi wurin mai maganin gargajiyan nan, wato Maude, ita kuma Jane za ta gano wani hali na John wanda ba ta taɓa sani ba.

**Fitowa ta 4: A gidan John**

**Jane:** John! John! Ka tashi. Ya kamata mu shirya zuwa coci, ka ji? Ka san yau Laraba kuma ana addu'a ta musamman.

**John:** A'a Jane, ki wuce kawai. Yau ba na jin zuwa. Ki ce musu yau ba na jin daɗin jikina.

**Jane:** John, me kake nufi! Kana nufin in je in yi ƙarya? Da kana son irin wakokin kwaya da ake yi, me ya faru yanzu kuma? Don ka rasa aikinka ne? Haba John, mutane fa da yawa ba su da aiki kuma …

**John:** Jane, yau ba na jin zuwa coci, ki je kawai. Mako mai zuwa na je.

**Jane:** To in ce a yi maka addu'a? Ka san cewa za ka iya samun aikin da ya fi wanda ka bari a baya da.

**John:** Jane, ki yi duk abin da kika ga dama. Ni yanzu barci nake so in yi.

**Jane:** Gaskiya, ni ban gane maka ba, ba ka cin abinci sosai, sai ka yi ta dogon barci, ba ka jin daɗin irin abubuwan da da kake jin daɗinsu. Me ke damunka ne?

**John:** Ba wani abu! Don Allah ki kashe min wutar, sannan ki ja mun labulen windo, ba na son ganin haske.

**Jane:** Yanzu fa ƙarfe uku na rana. Sannan ka ce kana buƙatar duhu? Kana ba ni tsoro, John. Kana sa ni cikin damuwa matuƙa.

**Mai gabatarwa:**

Jane ta yi daidai idan har ta shiga cikin hali na damuwa. John na yin wasu abubuwa da ba ta gane masa ba, idan ta sha'anin kiwon lafiya ne, sai a ce ya shiga halin takaici. Amma me ake nufi da takaici? Yaya kuma za a ci gaba da labarin Musa da Amina? A kasance da mu a shiri na gaba don jin waɗannan amsoshi.

Idan kuna muradin sake saurаron shirin, sai a nemi adireshinmu na yanar gizo, wato dw.de/le. Ana kuma iya ziyartar shafinmu na Facebook domin tattaunawa a kan wannan shirin. Sai mun sadu a shiri na gaba. Ku huta lafiya.